# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na tara: Wa na aura?

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |
| Charles: | ɗan shekara 45 |
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |
| Matar M. Talle: | ’yar shekara 55 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. Wannan shi ne kashi na tara na wasan kwaikwaiyonmu mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”. A cikin shirin da ya gabata, kun ji yadda abubuwa ke tafiya a rayuwar Lami. Da ma dai tana cikin damuwa saboda ƙarancin kuɗin da yake damunta. Can kuma sai ga shi iyayenta sun yi mata waya suna shaida mata halin da suka shiga na sallamarsu da aka yi daga aiki. Don haka sai ta yanke shawarar amsa tayin da Sa’adatu ta yi mata na aiki a wani gidan rawa, kuma ma har ta fara tunanin yin auren biza, tana ganin yin hakan zai taimaka mata wajen samun takardar izinin yin aiki a Turai. Sai dai kuma abin tambaya a nan shi ne, ko Lami ta san sakamakon abin da take aikatawa kuwa?

Can kuma a ɗaya ɓangaren a Arewacin Afirka, ga alama Faisal da Suleman sun yi baram-baram, bayan da aka samu wani rikicin siyasa da ya kunno kai a cikin ƙasarsu. To ko za su daidaita a tsakaninsu kuwa? Ko kuwa wannan shi ne ƙarshen abotar tasu?

A wannan shirin namu na yau mai taken “Wa na aura?” za mu fara ne daga ofishin rijistar ma’aurata inda aka ɗaura wa Lami auren biza da wani mutum mai suna Charles, wanda ba ta san ma da zamansa ba a rayuwarta. Wannan auren dai Sa’adatu ce ta shirya shi.

**Fitowa ta 1: Lami da Charles a wajen rijistar ma’aurata**

**Sa’adatu:** Habawa! Lami, ai kin yi komai! Ina taya ki murna ke da Charles! Allah Ya ba da zaman lafiya.

**Lami:** Na gode.

**Charles:** Gaskiya ni dai tafiya zan yi, sai dai ku yi haƙuri. Ke Lami, yanzu dai kin zama amarsu ta ango, kuma ga shi kin fito fes da ke. Na san dai Sa’adatu duk ta yi miki bayanin yadda za a yi ko?

**Lami:** E, ta yi min. Ta ce zan dinga zuwa gidan aƙalla sau uku a sati don mu tabbatar wa da kowa cewa aurenmu na gaske ne, kuma zan dinga biyanka Yuro ɗari takwas duk wata.

**Charles:** Ya yi daidai! To, yanzu ga mukullan gidan nawa. Ki dinga kirana ko kuma ki yi min *text* idan za ki zo. Sai in ce Allah Ya ba da sa'a, kuma sai mun haɗu !

**Sa'adatu:** Da kyau, uwargidan Charles! Wai yaya kike ji yanzu a matsayinki na matar aure? Kuma yaya kika ga mijin naki?

**Lami:** Gaskiya Sa'adatu, na yi takaicin shiga cikin wannan harkar. Sai nake jin kaina kamar na zamo shugabar maciya amanar duniya. Duk sai nake jin na rasa inda kaina ma yake, ban san yadda aka yi harkar nan har aka gama ta ba. Wallahi har lokacin da aka zo dab da ɗaura auren, ba tunanin da nake yi sai, "Wai ni kuwa, wa zan aura?"

**Mai ba da labari:**
Lami dai ta iso Turai ne a matsayin yarinya saliha, kuma mai basira, wadda ba ta san halin da duniya take ciki ba. Amma yanzu ga shi cikin 'yan watanni kaɗan har an ɗaura mata aure da wani wanda ba su taɓa haɗuwa da shi ba. Ga shi kuma yanzu tana faman aiki na tsawon lokaci a wani gidan rawa don ta biya wannan mutum ladan taimaka matan da ya yi wajen samun takardar izinin yin aiki a Turai. Sai dai kuma ga alamu, Lami tana da farin jini a gun kwastomomi don kuwa suna ɗan yi mata alheri.
To, can kuma a gida Afirka, Magaji ya ɗan kwana biyu bai ji labarin Lami ba don haka ma har ya fara ɗan damuwa. Saboda ya samu kwanciyar hankali, sai ya yi tunanin zuwa wajen iyayenta domin su kaɗai ne kawai za su iya taimaka masa. Rannan da maraice sai ya kai musu ziyara, ga kuma yadda ta kasance:

**Fitowa ta 2:** **Magaji ya kai wa iyayen Lami ziyara**

**Malam Talle:** Maman Lami, duba ki ga wane ne a ƙofar gida, don na ga karen can ya dage da haushi. Idan ya ci gaba da irin wannan haushin kuma, lallai za mu kai shi gidan mahaukatan karnuka!

**Matar M. Talle:** Da gaske kake ko kuwa dai wasa kake? Bari dai na je na leƙa na ga ko wane ne. … Magaji! Shigo mana. Rabon da mu sa ka a idonmu tun ranar da Lami ta tafi Turai.

**Magaji:** Na san za ku ga ban sanar da ku ba, kawai na zo muku da yammaci, wallahi ba daɗewa zan yi ba. So nake kawai na ji labarin halin da Lami take ciki.

**Matar M. Talle:** To, shigo mana, ai kai ba baƙo ba ne! Ka manta nan gidanku ne? Ka manta cewa mu 'yan Afirka ne? Ai baƙonka Annabinka.

**Magaji:** To shi ke nan, na gode, Mama. Amma wallahi ba daɗewa zan yi ba.

**Malam Talle:** Magaji, ɗana na kaina! Yau kai ne da kanka ka ziyarce mu! Kana nan lafiya?

**Magaji:** Lafiya lau, Baba.

**Malam Talle:** Na ga kamar wani abu yana damunka. Allah Ya sa dai ƙalau?

**Magaji:** Lafiya lau wallahi! Gaskiya dai batun Lami ne ya kawo ni, Baba. Na yi kusan wata biyu ban ji labarinta ba. Kuma ni

ban san ta da haka ba. A farkon tafiyarta zuwa Turai mukan yi hira da ita a kullum. Yanzu na zo ne na ji ko kuna da labarin da ba ni da shi game da ita.

**Matar M. Talle:** To, bari na kyale ku, ku tattauna. Kai Magaji, bari na kawo maka shayi ka sha!

**Magaji:** Wallahi na gode, Mama. Ba daɗewa zan yi ba.

**Malam Talle:** Umh… Na ji kana cewa wata biyu ba ka ji labarin Lami ba ko?

**Magaji:** Kwarai kuwa. Yau wata biyu ke nan da kwana tara da kuma awa goma sha bakwai da daƙiƙa biyar. Amma dai ai tana lafiya ko?

**Malam Talle:** Lafiyata ƙalau. Sai dai kawai tana buƙatar ɗan lokaci ne don ta mai da hankali ga karatunta.

**Magaji:** Baba, ni fa na fahimci Lami sosai da sosai. Na san ba za ta taɓa yi min haka ba, idan ba... idan ba wani saurayin ta samu a Turai ba.

**Malam Talle:** A'a, ba haka ba ne. Tsaya ka ji, Magaji. Lami fa tana ƙaunarka, kuma idan ma ta samu wani saurayin, mu ya kamata a ce mun fara samun labari. Don ba ta ɓoye mana komai. Na yi ma magana da ita kwanan nan, kuma na ji tana nan a kan bakanta.

**Magaji:** To Baba, ka taimaka min da lambarta mana, ina son in yi magana da ita.

**Malam Talle:** Kusan zan iya cewa lamba ba tata ba ce, ta ƙawarta ce

wadda ake kira Sa'adatu. Ina jin tare suke karatu da ita duk da dai ban taɓa tambayarta ba.

**Magaji:** To don Allah, ko za ka ba ni lambar Sa'adatun?

**Malam Talle:** Me zai hana. Kuma idan ka buga mata ma, ka ce muna gaishe ta. Tsaya, bari na duba maka lambar a cikin wayata. … Yauwa, ga ta nan. Akwai biro a wajenka ka rubuta?

**Magaji:** Kwarai, akwai. … Na gode ƙwarai da gaske. Allah Ya ba mu alheri.

**Malam Talle:** Amm… Magaji, ba ka ji abin da Maman Lami ta faɗa ba ne ɗazu, cewa baƙi da alheri suke zuwa? Gaskiya zan gaya maka, wallahi a yanzu muna cikin wani hali na rashin kuɗi. Shi ne nake tunanin ko za ka ɗan ranta mana wasu 'yan kuɗi, nan da 'yan kwanaki. Ina fatan dai ka fahimce ni.

**Magaji:** Haba, me zai hana. Wallahi ban ji daɗin labarin ba. Lami ba ta taɓa gaya min ba. Yanzu ba ni da kuɗi sosai a jikina, amma bari in duba. … Yauwa, ga wannan, ba yawa. Kwa aiko min idan har akwai wani taimako da zan iya yi muku. Ba kuma bashi ba ne. Allah Ya ba mu alheri, Baba.

**Malam Talle:** Kai! Gaskiya, mun gode, Magaji! Ubangiji Allah saka da alheri.

**Magaji:** Amin, Baba.

**Malam Talle:** Mun gode! Sai da safe.

**Mai ba da labari:**

To, ga dai Magaji can yana ta juyayin halin da Malam Talle yake ciki. Duk da cewa ya damu saboda rashin samun labarin halin da Lami take ciki, amma labarin halin da iyayenta suka shiga na matsalar kuɗi ya fi ma komai muni. Kuma wani abin ɗaure kai shi ne, Lami ba ta taɓa gaya masa haka ba. To bayan da ya fito daga gidan su Lami, sai ya nufi shagon intanet don a nan ne zai yi kira zuwa ƙasashen waje cikin sauƙi. Yanzu bari mu koma Turai inda yanzu haka dare ya yi lokacin da Lami za ta fara aikinta a gidan rawa. Ga Sa'adatu can tare da ita suna shan lemo.

**Fitowa ta 3: Magaji ya kira Lami ta wayar Sa'adatu**

| | |
|---|---|
| **Sa'adatu:** | *Hello*, wa ke magana? |
| **Magaji:** | Alo, Sa'adatu ce? Sunana Magaji. Ni ne saurayin Lami. Na samu wannan lambar taki ce daga wurin babanta. Ya gaya min cewa ke ƙawarta ce a jami'a. Ko kuna tare da ita? Ina son za mu yi magana da ita. |
| **Sa'adatu:** | Magaji? E, muna tare. Da ma kai ne Magajin da ake faɗa? To tsaya ka ji, yanzu dai Lami tana kan aiki. |
| **Magaji:** | Wane kiɗa nake ji haka ta cikin waya? Wane aiki take yi haka har da ba za ta ba ni minti ɗaya mu yi magana ba? |
| **Sa'adatu:** | Ka cika tamabaya! Ni kuma ba na son yawan tambaya. Kuma ka san wani abu, jinina bai haɗu da naka ba. Ga wata shawara zan ba ka. Ka manta da Lami kawai, ka nemi wata! |
| **Magaji:** | Me kike cewa? Ke kuwa me kika taka kike faɗa min wannan maganar? To, tsaya ki ji, Sa'adatu ake ce miki ko ma mene |

ne: ni da Lami fa alƙawarin aure muka yi, ko kina so ko ba kya so.

**Sa'adatu:** Au, haka ma za ka ce min? To, shi ke nan, bari na ba ka ita. Sai ka ci gaba da mafarki! … Ke Lami, ga Magaji nan ya bugo miki waya.

**Lami:** Magaji kika ce? A ina ya samu wannan lambarki? Af, na san zancen, ina ganin babana ne ya ba shi. Gaya masa ba na nan!

**Sa'adatu:** Na riga na gaya masa. Amma fa cewa ya yi wai ke zai aura. Na san bai san kin riga kin yi aure ba.

**Lami:** Don Allah Sa'adatu, ki kashe wayar. Ni ba zan yi magana da shi ba yanzu. Gaskiya ban shirya ba.

**Sa'adatu:** Shi ke nan, sai yadda kika ce, uwargidan Charles.

**Lami:** Kin san wani abu kuwa Sa'adatu, ina ganin ya kamata na ziyarci gida, tun da na ɗan tara kuɗin da zai saya min tikiti. Ya kamata na samu ɗan hutu don na jima ban ga iyayena ba.

**Sa'adatu:** To shi ke nan. Amma fa ki tabbata kafin ki tafi kin biya Charles kuɗinsa. Kuma kin san ba zai wuce sati ɗaya ba za ki dawo. Ai kin gane ko?

**Lami:** E, na gane.

**Mai gabatarwa:**

To masu sauraro, a yayin da Lami ta ci gaba da aikinta na raba abin sha a

cikin wannan gidan rawa muka kawo ƙarshen wannan kashi a shirin namu na wasan kwaikwayo. Yanzu dai ta yanke shawarar komawa gida don ta yi hutun sati ɗaya. To, yaya za ta ji idan ta haɗu da iyayen nata da kuma saurayinta Magaji? Musamman da yake Sa'adatu ta shaida wa Magaji cewa ya manta da Lami ya nemi wata. Ko me zai yi don ya tabbatar da cewa wannan budurwa tasa da suka taso tare bata kuɓuce masa ba? A ɗaya ɓangaren kuma na arewacin Afirka, za mu so jin halin da Faisal yake ciki. Na san masu saurare ba su manta da shi ba. Da yake akwai rikicin siyasa a ƙasarsu, ko zai sake wani shirin na shiga Turai ba bisa ƙa'ida ba?

To idan kuna son jin yadda za ta kaya da ma sauransu, sai ku kasance da mu a shirinmu na gaba. Haka kuma za ku iya tuntuɓarmu a dandalin muharawa da musayar ra'ayi na Facebook, wato facebook.com/dw.lbe don tattauna batutuwa a kan ƙalubalen zamantakewa da 'yan Afirka ke fuskanta a Turai. Kafin nan sai mu ce, Allah Ya ba mu alheri, amin.